# Musulunci ya zama abin misali mai haske wajen cikin cigaban bil’adam. In ji Shekh Irimata Sabri

**Category : Hirar wata-wata**

**Published by** Admin on 2010/6/14



wanda ya yi hira da shi : Khalid bin Ramadhan

Shekh Irimata Sabri shugaban kungiyar koli ta Musulunci, kuma limamin masallacin kudus ya yaba da irin kokarin da jagoran JAMUD ke gudanarwa dangane da taimaka wa Palasdinawa a Gaza, yana mai jinjina masa bias yadda yake yake bibiyar batun nan Kudus, tun lokacin da aka kawo canjin Alfatih, yana mai nuni da cewa: “ Ina gaida Jagoran JAMUD bisa babban kokarin da yake yin a taimakon Palasdinawa a Gaza, wannan kuwa baa bin mamaki ba ne a wurin Jagoran al’umma wanwa yake ya zama zuciyar duniya, wanda yake lura da kudus, tun lokacin da aka kawo Canjin Alfatih na Musulunci” yana mai mika godiyarsa tare da jinjinawarsa bisa ayyukan da JKMD ke yi a fagen da’awa wanda ya mamaye duniya baki daya.

Hakan ya zo ne a hirar da shafin JKMD na intaten ya yi da shi, a gefen babban taron JAMUD karo na biyar wanda aka yi kwanakin baya a Tripoli.
Ga yadda hirar ta mu ta kasance :

Kudus kalma ce da ta zama kalmar siri a yayin gudanar da canjin Alfatih

- Jagoran JAMUD yana gudanar da ayyuka da dama saboda hidimta wa Musulunci da Musulmi, ta yaya kuke kallon wannan kokari ?
- Alal Hakika kokarin da Jagoran JAMUD ke yi na hidimta wa Musulunci da Musulmi suna da yawa, musamman ma sallolin jam’in da yake limantar jama’ar Musulmi da dama a kowace shekara yayin gudanar da mailidin Annabi (SAW) wanda ake gudanar a kasashen duniya da dama. Wadannan ayyuka suna zuwa ne a matsayin raddi ga masu yi wa Musulunci bace, kuma wadannan salloli suna nuna cewa lalle al’umma Musulmi tana nan da ranta tare da alherinta. Kuma addinin nan yana mazajen da za ku iya ba shi kariya, don ya samu daukaka tare da hada kan al’umma.
Kuma a gaskiya al’ummar Palasdinawa suna ganin girman Jagoran JAMUD tare nuna masa kauna, kuma suna bibiyar irin ayyukan da yake yi, haka nan sun san cewa Kudus ita ce kalmar sirri daren canjin Alftih, kuma wannan birni bai gushe yana cikin zuciyar Jagoran JAMUD, Palasdiwa kuma suna jinjina irin kokarin da jagoran ke yi wajen ceto Kudus daga kokarin da Yahudawa ke yi na yahudantara da ita, tare da mummunan yanayin da Gaza ke fama da shi.

Ta yaya za a iya fuskantar hare-haren da Sojin Sahayina ke kai wa kan masallacin Kudus ?
Mu muna riko da hadisin Annabi (SAW) da ke cewa: “Ka da nika garin tafiya sai wurare uku, Masallaci mai alfarma, wannan masallaci nawa, masallacin Kudus” wannan yana nufin cewa an dora wa Musulmi zuwa masallacin Kudus, saboda shi ne wurin isra’in Manzon Allah (SAW), kuma addininmu yana umartarmu da mu yi aiki don kare wannan masallaci.
Tafiya da zamani
Ta wadane hanyoyi ne za a daukaka ayyukan Musulunci
Don daukaka ayyukan Musulunci ya zama dole mu duba matsalolin da muke so mu magance su, kuma mu karanta tarihin Annabi (SAW), mu yi koyi da shi, abu na biyu kuma mu yi amfani da kayan zamani na takanolaji don ya taimaka mana wajen isar da ilimi cikin hanya mai sauki.
JKMD sun yi zurfi a fagen da’awa, ta yaya koke ganin wannan kokari ?
Mu muna yaba irin kokarin da JKMD ke yi a kasashen duniya daban-daban, musamma ma a Afurka, ina ma a ce dukkan kungiyoyin ayyukan alheri su yi ko yi da JKMD, saboda JKMD ta mamaye duniya da ayyukanta, wannan kuwa yana karfafa guiwar masu aikin da’awa don su ci gaba da ayyukansu, musamman a yankunan da ‘yan mishan suka yawaita.